# Alamar Hash

Mahalarta taron za su koyi yanda alamar hash ke yin tasiri wajen inganta ƙungiyoyi. Haka kuma mahalarta taron za su gane yanda alamar hash a dandalin sadarwar zamani ke taimakawa wajen wayar da kawunan jama'a game da rajin kawo sauyi a kan wata matsala da kuma yanda za su samar da tasu alamar hash ɗin da hanyoyin inganta wani sanadin da yake ba su sha'awa.

# Rajin Kawo Sauyi Ta Hanyar Yin Amfani da Alamar Hash a Rubutu

## Kashi na Ɗaya

### Sanar da Ɗalibanka

Yayin da mutane ke yin amfani da wasu ƙayyadaddun dandalin sadarwar zamani a kai a kai wajen wayar da kan jama'a wajen rajin kawo sauyi a kan wasu dalilai na musamman, waɗannan dandalin sadarwar zamanin suna da wasu halayya na bai ɗaya. Wata fitacciyar sifa guda ɗaya mai taimakawa ita ce alamar hash a rubutu. Alamar hash a rubutu na ba mu damar jawo hankali mutane ga ra'ayoyinmu ta hanyar haɗa aikenmu da wasu aiken a kan batu iri ɗaya. Misali, idan muna so mu raba bidiyoyi daga wasan ƙwallon ƙafarmu na kwanan nan a inda ɗan wasanmu ya ci ƙwallaye uku a wasa guda, za mu iya haɗawa da "#ƙwallon ƙafa" da "#ƙwallaye uku a wasa guda" a cikin bayanin da ke bidiyon don ba sauran mutanen da ke neman bidiyon ƙwallon ƙafa damar ganin shi. Ta wannan hanyar, za mu iya ƙara damar da ƙwararrun 'yan wasan suke da ita da za su duba bidiyoyinmu.

Alamar hash a rubutu suna da amfani musamman a ayyukan rajin kawo sauyi. Misali, bayan da wani jami'in 'yan sanda ya harbin Trayvon Martin a Florida, ta ƙasar Amurka, wasu 'yan rajin kawo sauyi da yawa suka fara rubuta aike game da dangantakar wariyar launin fata a Ƙasar Amurka sannan suka haɗa da alamar hash a rubutu #BlackLivesMatter. Ta hanyar ƙaruwar shaharar alamar hash a rubutu, mutane da yawa za su iya ganin aike game da ƙwarewar mutane a matsayin launin mutane da kuma kasancewarsu da 'yan sanda a Ƙasar Amurka yau ta hanyar binciko "#BlackLivesMatter." Ta hanyar rajin kawo sauyi a dandalin sadarwar zamani, muhimmancin Rayukan Baƙaƙen Fata ya bunƙasa zuwa wani rajin kawo sauyi mai ƙarfi ta hanyar goyon bayan mutane masu ƙarfi.

Alamar hash wani nau'in abu ne a dandalin sadarwar zamani a kan wani mizani a duniya. A lokacin da ƙungiyar 'yan ta'addan Boko Haram ta yi garkuwa da 'yan mata 276 daga makarantar sakandare a Chibok, Nijeriya, mutane a Nijeriya sun yi ƙokarin wayar da kawunan mutane dangane da matsalar a dandalin sadarwar zamani ta hanyar aikewa da abubuwa tare da alamar hash "#BringBackOurGirls." Matsalar ta tattara goyon bayan mutanen duniya cikin sauri, tare da fitattun 'yan wasa da kuma fitattun mutane da ke goyon bayan sanadin.

Akwai wasu misalai da yawa na yin amfani da alamar hash don rajin kawo sauyi a faɗin duniya. Misali, ɗaliban jami'ar Mexico sun yi amfani da "#YoSoy132" a zaɓen shugaban ƙasa na shekarar 2012, ɗaliban jami'ar Hong Kong sun dogara a kan alamar hash ɗin "#umbrellarevolution" a lokacin zanga-zangar domokaraɗiyya a shekarar 2014, kuma ɗaliban jami'ar Chilean sun yi amfani da "#MovimientoEstudiantil" don rajin kawo sauyi a harkar ilimi.

A lokacin da kake rajin kawo sauyi saboda wani sanadi, yin amfani da alamar hash

wata babbar hanyace ta kaiwa ga masu sauraro tare da ra'ayoyinka. A cikin waɗannan ayyukan, za mu bincika yanda ake yin amfani da alamar hash a dandalin sadarwar zamani.

# Aiki

## Kashi Na Ɗaya

**Tattaunawa a Aji**

Shirya maharta taron bibbiyu.

**Sanar da Ɗalibanka**

A cikin ƙungiyoyin masu mutane bibbiyu, nemo alamar hash ɗin da aka yi amfani da ita kwanan nan don inganta wani sanadin.

Da zarar ka nemo alamar hash ɗin, yi bitar firar da aka yi a wurin sannan kuma a cikin ƙungiyarka, samar da taƙaitaccen bayanin abun da aka tattauna. Za ka gabatar da wannan taƙaitaccen bayanin da baki ga sauran ƙungiyar.

Kana da mintuna 15 domin ka nemo alamar hash ɗin sannan ka samar da taƙaitaccen bayanin.

**Tattaunawa a Aji**

Ba mahalarta taron mintuna 15 don su yi aiki. Da zarar sun gama, ba kowace ƙungiya mai mutum bibbiyu mintuna 15 domin su gabatar da taƙaitaccen bayaninsu ga ƙungiyar.

**Tambayi Ɗalibanka**

Wane irin abu ne aka raba ta hanyar yin amfani da alamar hash?

Shin akwai wasu firarrakin da ake yi a ƙarƙashin waɗannan alamar hash ɗin mabambanta? Me yasa kake tunanin wannan yana faruwa/ba ya faruwa?

Shin wasu daga cikin alamar hash ɗin na aiki sosai (misali., za a iya sake aikewa da su) a kan sauran? Waɗanne? Me yasa?

## Kashi Na Biyu

**Sanar da Ɗalibanka**

Yanzu, samar da wani lamarin da yake da muhimmanci ga ƙungiyarka sannan ka:

1. Kirƙirar masa alamar hash.

2. Tsara wani hoto, bayani mai hoto, meme, taɗi, ko zane mai hoto domin inganta alamar hash ɗinka.

3. Tare da abokin hulɗarka, tattauna hanyoyi daban-daban da za ka yaɗa alamar hash ɗinka ta amfani da hanyar sadarwa. Wasu dabarun kaiwa ga nasara ne muka koya daga dudduba sauran alamar hash ɗin?

Za a ba ka mintuna 30 domin ka kammala wannan aikin.

**Tattaunawa a Aji**

Ba mahalarta taron mintuna 30 domin su kasance da wannan aikin tare da abokin hulɗarsu. Bayan nan, bayar da mintuna 20 ga kowane mutum bibbiyu domin su tattauna, tare da, babbar ƙungiyar, alamar hash ɗinsu, mai ɗauke da abubuwan da za a gani, da kuma ra’ayoyi game da yaɗa alamar hash ɗin.

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.